# Imanin ɗayanku ba ya cika har sai na kasance mafi soyuwa a gare shi sama da babansa da ‘ya’yansa da mutane bakiɗaya

An karbo daga Anas Allah Ya yarda da shi, ya ce: Ma'aikin Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: Imanin ɗayanku ba ya cika har sai na kasance mafi soyuwa a gare shi sama da babansa da ‘ya’yansa da mutane bakiɗaya.
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana ba mu labarin Musulmi ba zai kasance mai cikakken imani ba har sai ya gabatar da son Ma’aikin Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, a kan son babarsa da babansa da ɗansa da ‘yarsa da mutane bakiɗaya, wannan soyayya kuwa tana hukunta yi masa biyayya da taimaka masa da kuma barin saɓa masa.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC
E-Da'wah Committee